ARDP

# Rahoton

## Ayyukan Mazaɓun Tarayya a Jihar Zamfara Na Shekarar

# 2023

Supported by:

MacArthur Foundation

# GABATARWA

Bibiyar ayyukan mazaɓu a jihar Zamfara na ɗaya daga cikin ayyukan ƙungiyar Nazari da Ƙoƙarin Ciyar da Arewa Gaba (ARDP); a matsayin ɗaya daga cikin shirye-shiryen da gidauniyar MacArthur ke tallafamawa a ƙarƙashin shiri mai take da "On Nigeria 2.0". Manufofin shirin sun mayar da hankali ne kan rage cin hanci da rashawa ta hanyar taimaka wa shirye shirye da yunƙurin al'umma da za su ƙarfafa al'adar riƙon amana, gaskiya da kuma sa hannun jama'a wajen gudanar da al'amuransu. Ɗaya daga cikin manyan maƙasudin wannan aiki shi ne tantance matakan shigar da al'ummomi dabandaban wajen ƙirƙirowa da aiwatar da ayyukan mazaɓu da nasabarsu da bukatun al'umma. Har ila yau, ana sa ran aikin zai samar da tsari ko kuma ƙara sa ƙaimi ga 'yan kasa wajen ƙirkiro da ayyukan mazaɓu da kuma zaburar da al'umma wajen sa ido da bin diddiƙin ayyukan. Wannan aikin ƙungiyar ZamTracka ce, abokiyar hadin gwiwa a jihar Zamfara, ke aiwatarwa.

Ƙungiyar ARDP dai wata cibiya ce mai bincike da bata da alaƙa da gwamnati ko la'akari da wata siyasa, ƙabila, ko nuna bambancin addini wadda ayyukanta sun mayar da hankali wajen nazari da tantance manyan matsaloli da ke addabar Arewacin Nijeriya da al'ummarta, da yunƙurin samar da hanyoyin bincike da tsare-tsaren ayyukan da zasu magance matsalolin dake addabar yankin. Gurin Cibiyar shine ƙoƙarin samar da tafarkin bunƙasar tattalin arziki da kyautata rayuwar al'ummar yankin ta hanyoyin da zasu samar da haɗin guiwa tsakanin jama'a da hukomomin gwamnati wajen hada ƙarfi-da-ƙarfe domin ciyar da al'umma gaba.

Ita kuwa ZamTracka, ƙungiya ce mai zaman kan ta da ke Gusau a jihar Zamfar, wadda ta ke yekuwar ganin ana yin taka tsan-tsan da dukiyar jama'a a cikin mulkin jihar. Fitattun ayyukan ta sune samowa da tantance bayanai kan tanade tanaden ayyuka da ke cikin kasafin kuɗi na jihar Zamfara da kuma ayyukan raya-ƙasa a yankunan mazaɓu, da kuma yin amfani da su wajen wayar da kan al'umma. Manufa dai ita ce a taimaka wa jama'a wajen bin diddiƙin tanade-tanade kasafin kuɗi da yadda ake gudanar da ayyukan raya-ƙasa a mazaɓu. Ana san ran cewa wannan yunƙuri zai sa a samu masu himma da dagewa wajen ganin ana gudanar da ayyukan raya-ƙasa na gwamnati da hukumominta tare da haɗaka yadda jama'a za su nemi samun ɗorarriyar hanyar tsoma bakinsu a cikin gudanar da al'amuran jiharsu.

Ayyuka na shiyya, wanda aka fi sani da ayyukan mazaɓu, ayyuka ne na jama’a da ‘yan majalisar tarayya sukan gabar domin kawo ribar mulkin demokaraɗiyya ga al'ummominsu don haɓakar ci-gaban yankunan karkara. A kan gabatar da bukatun gudanar da waɗannan ayyukan ne ga sashen mulki a lokacin da ake tsare-tsaren kasafin kuɗi. Tsarin mulkin ƙasa ya tanadi cewa majalisun tarayya ke da alhakin sanya ido akan ayyukan gwamnati. Kasancewar 'yan majalisu ne ke ƙirƙirar ayyukan, ashe su ke da nauyin su riƙa yiwa jama'a bayanai akai-akai akan ayyukan. Wannan ya isa hujja saboda talakawa ba za su iya tunkarar hukumomin gwamnati cikin sauƙi ba kamar yadda za su iya tuntuɓar wakilan su. Domin ganin munbi diddiƙin waɗannan ayyukan raya ƙasa akan kari, mun yi amfani da jami'an mu waɗanda suka san wuraren da ake gudanar da takamaiman ayyukan.

A shekarar 2023, an ware jimillar Naira Biliyan 1.44 don gudanar da ayyukan mazaɓu a Zamfara, wanda mafi yawansu ya shadi horaswa ne da bada tallafin karfafawa jinsunan al'umma. Manyan ayyuka sun haɗa da samar da abubuwan more rayuwa na zahiri, kamar gina hanyoyi ko makarantu, yayin da ayyukan horaswa da tallafi suka fi mayar da hankali kan haɓaka ƙwarewa da iya aiki a cikin al'umma. A jihar Zamfara, manyan ayyuka na iya bada gudummawa ga inganta tsarin ababen more rayuwa, yayin da ayyukan horaswa da tallafi ke nufin ƙarfafa mutane da haɓaka ci gaba mai dorewa ta hanyar gina fasaha da ilimin su. Dukansu suna taka muhimmiyar rawa a cikin ci gaban al'umma, ta hanyar magance fannoni dabandaban na ginuwar al'umma. Sai dai babban abin da ke faruwa a jihar Zamfara shi ne, ayyukan horarwa da tallafi ba'a ƙiƙirosu da gudanar da su ta hanyar da za a cimma alfanunsu.

# MAZAƁAR GUSAU/TSAFE

**Hon. Kabiru Amadu**



**01**

Ayyukan da aka Gabatar

**01**

An Aiwatar

**0%**

Ayyukan Horo da Tallafi

**00**

Ba' a a yi ba

**100%**

Manyan Ayyuka

# Samar da fitulun sola (masu aiki da hasken ran) domin bunƙasa ayyukan noma a mazaɓar tarayya ta Gusau/Tsafe

An fara aikin ne a ranar 21 ga Disamba, 2023, kuma an ci gaba da aiwatar wa zuwa cikin watan Janairun 2024. Aikin ya shafi wurare guda uku ne: Unguwan Yarima a Gusau, Wanzamai, da kuma unguwar da ke kusa da Babban Asibitin Tsafe.

Masu tantance ayyuka sun gano muhimman batutuwa tare da aiwatar da wannan aikin. Kodayake taken aikin yana nuna haɓaka ayyukan noma da wasu ayyukan da suke da alaƙa da noma a cikin mazaɓar, wuraren da aka zaɓa ba su dace da wannan manufa ba. Musamman Unguwan Yarima, inda ɗan majalisar yake zaune, birni ne da ba wani aikin noma a wurin. Haka ma sauran wuraren basu cancanci samu tallafin da taken shirin ya ƙudurta ba.

Bugu da ƙari, aikin ya ƙunshi kafa fitilun hasken rana hamsin da biyu a dukan wuraren. Unguwan Yarima ta samu mafi rinjaye, na fitilu talatin, yayin da sauran ashirin da biyu aka raba tsakanin sauran wurare biyu a Tsafe. Binciken kasafin kuɗin aikin ya nuna rashin daidaituwa tsakanin kudaden da aka ware da na ainihin abin da aka kashe, wanda hakan ke nuna akasin kimar aikin.

A ƙarshe, sakamakon aikin dai ya kasance na ƙawata wurare ne, amma ba haɓaka aikin noma a mazaɓar ba. Wannan saɓani ya lalata tasirin aikin da aka yi niyya. Bugu da ƙari, har yanzu ba a san ko akwai ƙaƙƙarfan tsarin sa ido ko kula da aikin ba don magance matsalolin da ke tattare da fitilun titi.

Mazabar Gusau/ Tsafe

N121m

An Aiwatar !








# MAZAƁAR BUNGUDU/MARU

## Hon. AbdulMalik Zubairu



**04**
Ayyukan da aka Gabatar

**02**
An Aiwatar

**100%**
Ayyukan Horo da Tallafi

**02**
Ba a yi ba

**0%**
Manyan Ayyuka

# Samar da kujeru da tebura ga wasu makarantun firamare da ke mazaɓar tarayya ta Maru/Bungudu

Mazabar Maru/ Bungudu

**N21m** **An Aiwatar**

Dan majalisar na yanzu, wanda ya maye gurbin mai ci a zabukan 2023, ya gaji wannan aiki ne daga magabacinsa. Duk da sauyin da aka samu na gudanarwa, an yi nasarar aiwatar da wannan aikin.

Wannan aiki ya zo da wani sabon salo inda aka haɗa tebur da wurin zaman 'yan makaranta maimakon amfani da kujeru da tebura daban daban. An samar da wannan sabon tsarin a cikin makarantun firamare guda goma na mazabar, inda kowannensu ya karɓi tebura masu haɗe da kujera guda hamsin.

Masu tantance ayyuka, bayan sun ziyarci wasu makarantun da suka amfana, sun ba da rahoton wani gagarumin sauyi na magance ƙarancin wurin zaman 'yan makaranta. A can baya, ko dai yara su cunkushe a adadin kujerun da ake da su ko kuma a tilas su zauna a kan daɓen azuzuwa. Yanzu, suna da sarari wuraren zama na kujera da teburi. Ana sa ran wannan ci gaban zai inganta yanayin ilimi, ta yadda zai inganta koyarwa da koyo.













## Samar da injunan ɗinki ga mata a mazaɓar tarayya ta Maru/Bungudu

Mazabar Maru/ Bungudu

N25m An Aiwatar

An tsara wannan aikin ne musamman don tallafa wa masu sana'ar ɗinki ta hanyar kungiyarsu a ƙananan hukumomi biyu na mazaɓar. An ƙaddamar da shirin ne a ranar 14 ga Janairu, 2024, a ƙaramar hukumar Bungudu, inda masu sana'ar dinki tamanin da hudu – galibinsu mata – kowannensu ta samu sabon injin ɗinki.

Muhimmin al'amari na wannan aikin shine cikakken tsarin zaɓin masu cin gajiyar, wanda ya tabbatar da cewa an zaɓi waɗanda suka dace ne. Wannan tsarin na nuna alamar cewa waɗanda suka ci gajiyar za su iya riƙe kuma su yi amfani da sabbin injinan su yadda ya kamata don haɓaka sana'arsu.

Kasancewar daga ƙungiyar teloli ce aka zaɓi waɗanda suka ci gajiyar shirin zai ba da damar ingantaccen tsarin sa ido da kimanta tasirin shirin a gaba. Wannan tsarin yana iya haɓaka yuwuwar ci gaba da tallafawa da bunƙasa ga al'ummar teloli.













# Bada horo a kan sana'o'i da suka shafi amfanin noma da jari ga mata da matasa a mazaɓar tarayya ta Maru/Bungudu

Mazabar Maru/ Bungudu

**N50m** **Ba a yi ba**

Masu tantance ayyuka sun gudanar da cikakken bincike a faɗin mazaɓar domin tabbatar da aiwatar da wannan aiki. Amma, duk bayanan da aka tattara sun nuna akasin hakan. Daki-dakin rahotanni daga mutanen mazaɓar sun nuna ba'a aiwatar da aikin ba, wanda hakan a nan ke nuna wani gagarumin bambanci tsakanin aikin da aka tsara da kuma sakamakon aiwatar da shi a bayyane.

## Samar da hatsi a mazaɓar tarayya ta Maru/Bungudu

Mazabar Maru/ Bungudu

N25m

Ba a yi ba

Masu tantance ayyuka sun gudanar da cikakken bincike a faɗin mazaɓar domin tabbatar da aiwatar da wannan aiki. Amma, duk bayanan da aka tattara sun nuna akasin hakan. Daki-dakin rahotanni daga mutanen mazaɓar sun nuna ba'a aiwatar da aikin ba, wanda hakan a nan ke nuna wani gagarumin bambanci tsakanin aikin da aka tsara da kuma sakamakon aiwatar da shi a bayyane.

# MAZAƁAR BAKURA/MARADUN

## Hon. Muhammad Ahmed



**03**
Ayyukan da aka Gabatar

**02**
An Aiwatar

**75%**
Ayyukan Horo da Tallafi

**01**
Ba a yi ba

**25%**
Manyan ayyuka

# Horas da matan karkara wajen amfani da na'urar da ke amfani da makamashin zamani na sarrafawa da adana kayan abinci a mazaɓar tarayya ta Bakura/ Maradun

Mazabar Bakura/ Maradun

N40m

An Aiwatar

Ɗan majalisar, bayan ya ƙwace kujera a zabukan 2023, ya gaji wannan aiki daga magabacinsa. Ko da yake an aiwatar da aikin, amma ba tare da tagomashi ba. An ƙaddamar da aikin ne a ranar 19 ga Maris a Kwalejin Kimiyyar Noma da ke Karamar Hukumar Bakura. An horar da waɗanda suka ci gajiyar aikin guda hamsin (50), inda kowannen su ya sami tallafi na N20,000 tare da takardar shedar horo.

Musamman, akwai rashin daidaituwa tsakanin yadda aka tsara aikin da kuma yadda aka aiwatar da shi. Horon ya shafi mahalarta maza ne kawai, ba tare da shigar da mata ba, kuma ya mayar da hankali ne kawai kan fasahar hasken rana maimakon amfani da makamashi na zamani don sarrafa abinci da adanawa kamar yadda aka nufa da farko. Haka kuma, horon ya dauki tsawon kwana daya kacal, sabanin kwanaki shida da aka tallata a tutar aikin. Waɗannan bambance-bambancen suna nuna cewa an yi watsi da aikin da aka zaɓa na farko don neman wani tsari daban-maras manufa da inganci.

Idan aka yi la'akari da karkacewa daga shirin da aka tsara da kuma rashin aiwatar da aikin kamar yadda ya ke a tsare, ana iya cewa kwalliya ba ta biya kuɗin sabulu ba. Wannan yana nuna rashin yuwuwar samun tasirin shirin ta yadda duk wani ƙokarin auna ingancin sa ya zama aikin banza.









# Samar da fitilun titi masu amfani da hasken rana a mazabar tarayya ta Bakura/Maradun

Mazabar Bakura/ Maradun

N51m

An Aiwatar

An fara aikin sanya fitilun kan titi a ranar 21 ga Disamba, 2023. Ya zuwa lokacin da aka shirya wannan rahoton, ba a iya samun daidatuwar ainihin adadin fitilun da aka samar ba. Duk da haka, masu bin diddiƙin ayyuka sun yi nasarar fayyace wasu wuraren da suka ci gajiyar aikin don tantance tasirin aikin akan muhimman bukatu ko ƙalubalen da al'ummar ke fuskanta.

Ra'ayoyin al'ummar ya kasance mai daɗin ji. Yawancin wuraren da suka ci gajiyar shirin suna da matuƙar damuwa da yanayin tsaro a cikin dare, kuma ƙarin hasken da fitilun tituna ke bayarwa yana da fa'ida wajen inganta yanayin tsaro. Wannan ci gaban yana da mahimmanci musamman idan aka yi la'akari da tabarbarewar yanayin tsaro, saboda yana taimakawa wajen haskaka wurare, ciki da kewaye. Fitattun wuraren da suka samu hasken fitilun sun haɗa da masallatai, makarantun Islamiyya, kasuwanni, da shiyyoyi cikin yankunan karkara.

Duk da haka, babu tabbas na wani tsarin sa ido da kuma kula da aikin don tabbatar da ci gaba da kulawa da gyaran fitilun titi. Wannan rashin tsarin yana haifar da damuwa game da dorewar ingancin aikin.













## Gina rijiyoyin burtsatse masu amfani da hasken rana guda biyu a mazabar tarayya ta Bakura/Maradun

Mazabar Bakura/ Maradun

N30m

Ba a yi ba

Masu tantance ayyuka sun gudanar da cikakken bincike a faɗin mazaɓar domin tabbatar da aiwatar da wannan aiki. Amma, duk bayanan da aka tattara sun nuna akasin hakan. Daki-dakin rahotanni daga mutanen mazaɓar sun nuna ba'a aiwatar da aikin ba, wanda hakan a nan ke nuna wani gagarumin bambanci tsakanin aikin da aka tsara da kuma sakamakon aiwatar da shi a bayyane.

# MAZAƁAR ZAMFARA TA YAMMA

**Sen. AbdulAziz Yari**



**01**

**Ayyuakan da aka Gabatar**

**01**

**An Aiwatar**

**0%**

**Ayyukan Bada Horo da Tallafi**

**00**

**Ba a yi ba**

**100%**

**Manyan Ayyuka**

# Samarwa da sanya fitilun haskaka hanyoyi masu aiki da hasken rana domin haɓaka amfanin kayan noma a mazaɓar ɗan majalisar dattijawa ta Zamfara ta Yamma

Zamfara ta Yamma

N214m An Aiwatar !

Dan majalisar, bayan ya samu nasarar zama ɗan majalisar dattijawa a zabukan 2023, ya gaji wannan aiki daga magabacinsa. An aiwatar da aikin daga Disamba 2023 zuwa Janairu 2024. Har lokacin haɗa wannan rahoto, ba a iya samun daidaituwar ainihin adadin fitilun tituna da aka sanya ba.

Masu tantance ayyuka sun gudanar da bincike bukatun al'umma a wurare da su kaci gajiyar wannan aikin, waɗanda suka haɗa da Titin 'yar Yelwa, Titin 'Yar Hudu, 'Yan Kifi, yankin Karfi, 'Yar Zamau, da filin wasa da ke Titin, duk a mazaɓar. Manufar ita ce a tantance ko wannan aikin ya haɓaka ko inganta amfanin kayan noma kamar yadda taken aikin ya ƙudurta. Sakamakon ra'ayoyin al'ummar ya nuna akasin hakan. Galibin wuraren da suka amfana da shirin sun kasance birane ne, wanda hakan ya sa yana da wahala a haɗa su da duk wani muhimmin aikin noma. Don haka, a bayyane yake cewa aikin na ƙawata shiyyoyin gari ne domin haskaka wuraren a maimakon haɓaka ayyukan amfanin noma a yankunan.

Bugu da ƙari, har yanzu babu tabbas ko akwai tsarin sa ido da kulawa don na yau da kullun da gyaran fitilun tituna, wanda hakan ke haifar da damuwa game da ɗorewar ingancin aikin na dogon lokaci.








# MAZAƁAR GUMMI/BUKKUYUM

**Hon. Sulaiman Abubakar**



**03**

**Ayyukan da Aka Gabatar**

**02**

**An Aiwatar**

**75%**

**Ayyukan horo da Tallafi**

**01**

**Ba a yi ba**

**25%**

**Manyan Ayyuka**

# Kammala aikin cibiyar kiwon lafiya a Gamji a mazaɓar tarayya ta Gummi/Bukkuyum

Wannan aikin na cibiyar kula da lafiya mai gadaje talatin da ɗaya (31) da ke unguwar Gamji a gundumar Illela a cikin ƙaramar hukumar Gummi, an fara shi ne a watan Nuwamba 2020 amma an yi watsi da shi sama da shekaru uku. Wannan aikin na da nufin kammala cibiyar ne don amfanin jama'a.

Masu tantance ayyuka da ke bin diddiƙin aikin sun bayar da rahoton cewa an kammala aikin gine-ginen sai fenti kawai ya rage. Sai dai, a halin yanzu ba a san lokacin da za a kammala aikin gaba ɗaya ba domin a buɗe wa amfanin jama'a.

Idan aka yi la'akari da da yanayin da al'ummar garin da kewayenta suke ciki, da zarar an fara aiki, wannan cibiyar kiwon lafiya za ta kasance itace babbar cibiyar kula da lafiya a yankin, da ke kula da marasa lafiya daga wurare masu nisa. Sakamakon yuwuwar tasirin wannan wurin akan samun damar kula da lafiya na gida yana da mahimmanci.

Duk da haka, sau da yawa irin waɗannan ayyukan tallafi su kan kasa cimma manufarsu saboda rashin sa hannun jagororin al'umma da manyan masu ruwa da tsaki wajen gudanarwa da kula da ayyukan. Ana fatar wannan aikin zai kasance da ban, tare da sa hannun al'umma domin tabbatar da dorewar wannan cibiyar kiwon lafiya.

Mazabar Gummi/ Bukkuyun

N31m

An Aiwatar








# Samar da motar bos mai ɗaukar mutum 18 a mazaɓar tarayya ta Gummi/Bukkuyum

An sanar da samar da motar bas mai ɗaukar mutane goma sha takwas (18) a ranar 16 ga Maris, 2024, a wani biki da aka gudanar a ofishin dan majalisar da ke ƙaramar hukumar Gummi. A yayin wannan taron, an kuma bayyana akalla wasu motoci guda 10, duk da cewa an raba su a tsakanin wasu da aka ayyana masu biyayya ga dan majalisar.

Motar bas mai ɗaukar mutum goma sha takwas (18), wacce ke dauke da sitika da ke nuni da amfani da ita a matsayin ta hidimar al'amuran dalibai na mazabar, ta tada tambayoyi da dama. Ba a iya fayyace wajabcin sayen wannan motar, da kuma mai haƙƙin kula da da ita yau da kullum, da kuma tsarin yin amfani da motar ba. Waɗannan tambayoyi sun samo asali ne daga abubuwan da suka faru a baya tare da irin wannan, inda motocin da aka yi niyya don amfanin jama'a sun ƙare ga amfani ɗan majalisa, ba tare da yin amfani ga al'umma ba. A wani salon irin wannan a bara inda aka yi la'akari da wani aikin na sayen abin hawa da wani ɗan majalisar ya gabatar, amma ba a aiwatar da aikin ba.

Bugu da kari, kasafin kudin wannan aikin ya kai Naira miliyan 50, wanda ya nuna ya wuce gona da iri idan aka yi la'akari da yanayin motar. Binciken da aka gudanar ya nuna cewa farashin mota ƙirar Toyota mai ɗaukar mutum goma sha takwas (18) ta na tsakanin Naira miliyan 27 zuwa Naira miliyan 29, amma bas din da aka sawo wadda ta ji jiki ce. Wannan bambance-bambancen yana nuna rashin kula da dukiyar al'umma ta yadda kwalliya bata biyan kuɗin sabulu.

Mazabar Gummi/ Bukkuyun

**N50m** **An Aiwatar**










## Ɓunƙasa hanyoyin sarrafa kayan noma domin haɓaka hada-hadar kasuwanci da ƙarfafama 'yan kasuwa a mazaɓar tarayya ta Gummi/Bukkuyum

Mazabar Gummi/ Bukkuyun

N40m | Ba ayi ba

Masu tantance ayyuka sun gudanar da cikakken bincike a faɗin mazaɓar domin tabbatar da aiwatar da wannan aiki. Amma, duk bayanan da aka tattara sun nuna akasin hakan. Daki-dakin rahotanni daga mutanen mazaɓar sun nuna ba'a aiwatar da aikin ba, wanda hakan a nan ke nuna wani gagarumin bambanci tsakanin aikin da aka tsara da kuma sakamakon aiwatar da shi a bayyane.

# MAZAƁAR KAURA/BIRNIN MAGAJI

**Hon. Aminu Sani Jaji**



**02**

**Ayyukan da Aka Gabatar**

**02**

**An aiwatar**

**100%**

**Ayyukan Horo da Tallafi**

**00**

**Ba a yi ba**

**0%**

**Manyan Ayyuka**

# Koya ayyukan sana'a ga matasa da mata a mazaɓar tarayya ta Kaura/Nirnin Magaji

Dan majalisar wanda ya karɓi ragamar mulki bayan zaben 2023, ya gaji wannan aiki wanda aka na tsawon kwanaki biyu, daga ranar 17 zuwa 19 ga watan Yuli, 2023, a Kwalejin Kimiyya da Fasaha ta Tarayya da ke Kaura Namoda. Aikin ya ƙunshi horar da mutane ɗari (100) daga gundumomi ashirin da daya na mazabar a fannin yin sabulu da man shafawa. Kowane daga waɗanda suka ci gajiyar aiki ya/ta sami takardar shedar halarta da tallafin N15,000 a matsayin jarin fara aikin don bunƙasa ƙananan kasuwanci.

Kodayake, bisa ga abubuwan da aka lura da su a ayyuka irin waɗannan a baya, yana da matuƙar wahala wajen tantance tasirin aikin. Sau da yawa, waɗanda suka dace—waɗanda za su iya amfana da gaske daga irin wannan horon—ba su ne waɗanda ake koya musu ba. Bugu da ƙari, rashin tsarin sa ido da bin sawun shirin, yana da wuya a tantance tasirin aikin a kan mahalartan da kuma a cikin al'umma gabaɗaya. Sabili da haka, yawancin waɗanda a ka horas ba aikin ne ke gabansu ba, amma kuɗin tallafi da zasu samu don buƙatun yau.

Don haka, yana da mahimmanci irin waɗannan ayyukan su mayar da hankali kan zaɓar mutanen da suka dace domin horaswa kuma sa samar da ingantaccen tsari don sa ido da bibiyar tasirin shirin. Wannan hanya ce za ta taimaka wajen tabbatar da cewa ayyukan sun sami tasiri mai ɗorewa daidai da manufofin ayyukan.

Mazabar Kaura/Birnin Magaji

**N25m** **An Aiwatar** !














# Samar da iri-iren ayyukan aikin noma a mazaɓar tarayya ta Kaura/Birnin Magaji

Dan majalisar, wanda ya yi nasarar hawa kujera bayan zabukan 2023, ya gaji wannan aiki ne daga magabacinsa kuma ya aiwatar da shi a ranar 17 ga Yuli, 2023, a Kwalejin Kimiyya da Fasaha ta Tarayya, Kaura Namoda. Musamman ma, an fara wannan aikin a rana ɗaya ne da wani shirin makamancin haka.

Yayin da har yanzu ba a fayyace adadin waɗanda suka ci gajiyar tallafin ba, an ruwaito cewa manoma ne na zahiri da ke wakiltar kowace gundumomi ashirin da ɗaya na mazabar. Idan aka yi la’akari da yanayin ayyukan noma a mazaɓa za a iya cewa duk wani shirin haɓaka aikin noma na da mahimmanci. Duk da haka, tallafin da aka bayar ta hanyar wannan aikin - na bai wa kowane mai cin gajiyar buhun taki guda kacal - ba zai iya magance bukatun manomi ba kuma ya gaza wajen bunƙasa ayyukan noma a yankin. Wannan yana haifar da damuwa game da wadata da ingancin taimakon da aka bayar ga wannan shiri.

Mazabar Kaura/Birnin Magajji

N50m

An aiwatar














# MAZAƁAR SHINKAFI/ZURMI

**Hon. Bello Hassan**



**03**

**Ayyukan da Aka Gabatar**

**03**

**An Aiwatar**

**75%**

**Ayyukan Horo da Tallafi**

**00**

**Ba a yi ba**

**25%**

**Manyan Ayyuka**

# Gyare-gyare da gina magudanun ruwa a garin Shinkafi cikin mazaɓar tarayya ta Shinkafi/Zurmi

An fara aikin ne daga ranar 12 ga Nuwamba, 2023, wanda ya shafi al'ummomi masu fama da ɓarɓashin zaizayar ƙasa da kuma kwazazzabun da ruwa ke taruwa a cikinsu a wasu gundumomi da dama na ƙaramar hukumar Shinkafi. Aikin gina magudanun wanda da aka yi amfani da siminti da karfe yana da alamar gamsarwa. Duk da haka, akwai damuwa game da rashin zurfin magudanar ruwa wanda hakan zai iya haifar da ambaliya a lokacin da a ka yi ruwan sama mai yawa.

Bugu da ƙari, rashin rufe magudanar ruwa na iya haifar da haɗarin zama wuraren ƙyanƙyasar sauro, wanda hakan zai iya ƙara yaduwar cutar zazzabin cizon sauro, sai dai idan ana share su da kula da su yadda ya kamata. An kammala wannan aikin in banda unguwar Katuru wadda ita ce kaɗai shiyyar da ba a kammala aikin magudanun ruwan ba.

Gabaɗaya, wannan aikin na da tasiri a mazaɓar. A zamanin sauyin yanayi lokacin da yanayin ruwan sama na iya zama maras tabbas, irin waɗannan gyare-gyaren muhalli na da mahimmanci don magance ƙalubalen da al'umma ke iya fuskanta a wuraren zamansu.

Mazabar Shinkafi/ Zurmi

N100m An Aiwatar








# Samar da tukunyar makamashin iskar gas a mazaɓar tarayya ta Shinkafi/Zurmi

Wannan aikin, wanda aka gudanar a ranar 17 ga Yuni, 2023, wani shiri ne na tallafawa kananan 'yan kasuwa a mazabar, sabanin samar da silinda gas kawai. An zaɓo mutane ɗari da tamanin 180 daga gundumomi ashirin da daya na mazabar: Shinkafi ta Arewa, Shinkafi ta Kudu, da kuma yankin Zurmi inda kowacce ta ba da gudummawar masu amfana goma sha biyu, yayin da sauran gundumomi goma sha takwas suka bayar da takwas kowacce. Wadannan mutane sun haɗa da masu sayar da shayi da biredi, masu sayar da wainar wake, da masu sayar da waken waken soya.

A ranar da aka ƙaddamar da shirin, an raba kayayyaki daban-daban don tallafa wa waɗannan ƙananan 'yan kasuwa akan kasuwancinsu. Kayayyakin sun haɗa da kwalayen na taliya, galan na man gyada, buhunan wake, manyan kwanin suya, da kuma tukunyar iskar makamashin gas mai nauyin kilo uku. Wannan hanyar tallafin kasuwanci na zahiri a maimakon tsabar kuɗi an tsara shi don hana karkatar da kuɗin zuwa amfanin da ba na kasuwanci ba. Hakan kuma na nufin samun ci gaba mai ɗorewa ga 'yan kasuwar da su ka ci gajiyar shirin.

Duk da yuwuwar aikin na iya yin tasiri mai ma'ana, babu tabbas ko akwai tsarin sa ido da bin diddiƙin tasiri da kalubalen da shirin zai iya fuskanta domin samun hanyoyin ɗorewar ingancin shirin na tsawon lokaci.

Mazabar Shinkafi/ Zurmi

**N21m** **An Aiwatar**









# Ƙarfafa matsayin ilimi ga ɗaliban mazaɓar tarayya ta ṣhinkafi/Zurmi

An ƙaddamar da wannan aikin ne bayan ƙara kuɗaɗen makaranta da manyan makarantu da jami'o'in gwamnati suka yi domin tallafawa ɗaliban ƙaramar hukumar da ke baya wajen ci gaban ilimi a cikin jihar. Manufar shirin shine na taimaka wa waɗanda suka sami damar yin karatu a manyan makarantu—wanda ke da mahimmanci idan aka yi la'akari da matsayin mazaɓar.

Kodayake, tsarin aiwatarwa na wannan shirin ya kasance a duƙunƙune. Masu tantance ayyuka ba su iya fayyace adadin kuɗin da kowane ɗalibi-mai cin gajiyar ya samu ba, wanda hakan ya sa yana da wahala a tantance ko an rarraba tallafin kuɗin daidai wa daida ga duk masu karɓa. Bugu da ƙari, ƙa'idodin da aka yi amfani da su don zaɓar waɗanda suka ci gajiyar da jimillar ɗaliban da tsarin ke tallafawa ba su fito fili ba.


Masu tantancewa sun samu takardun jerin sunayen waɗanda suka amfana daga Jami'ar Usmanu Danfodio da ke Sakkwato, wanda ke ɗauke da bayanai game da daliban. Duk da haka, har yanzu babu tabbas ko wasu jami'o'i ko cibiyoyin karatu suna cikin wannan shirin tallafi. Wannan rashin cikakken bayani ya gurgunta duk wani yunƙuri na kimanta tasiri da ingancin shirin.


Mazabar Shinkafi/ Zurmi


N50m


An aiwatar

!









# MAZAƁAR ZAMFARA TA AREWA

**Sen. Sahabi Ya'u**



**02**

**Ayyukan da Aka Gabatar**

**00**

**An Aiwatar**

**100%**

**Ayyukan Horo da Tallafi**

**02**

**Ba a yi ba**

**0%**

**Manyan Ayyuka**

# Tallafawa mata da matasa na mazaɓar ɗan majalisar dattijawa ta Zamfara ta Arewa

N100m Ba ayi ba

Masu tantance ayyuka sun gudanar da cikakken bincike a faɗin mazaɓar domin tabbatar da aiwatar da wannan aiki. Amma, duk bayanan da aka tattara sun nuna akasin hakan. Daki-dakin rahotanni daga mutanen mazaɓar sun nuna ba'a aiwatar da aikin ba, wanda hakan a nan ke nuna wani gagarumin bambanci tsakanin aikin da aka tsara da kuma sakamakon aiwatar da shi a bayyane.

# Samar da kayayyakin noma ga ƙananan manoma a mazaɓar ɗan majalisar dattijawa na Zamfara ta Arewa

Masu tantance ayyuka sun gudanar da cikakken bincike a faɗin mazaɓar domin tabbatar da aiwatar da wannan aiki. Amma, duk bayanan da aka tattara sun nuna akasin hakan. Daki-dakin rahotanni daga mutanen mazaɓar sun nuna ba'a aiwatar da aikin ba, wanda hakan a nan ke nuna wani gagarumin bambanci tsakanin aikin da aka tsara da kuma sakamakon aiwatar da shi a bayyane.

# MAZAƁAR ZAMFARA TA TSAKIYA

**Sen. Ikira Aliyu Bilbis**



**01**

**Ayyukan da Aka Gabatar**

**00**

**An Aiwatar**

**100%**

**Ayyukan Horo da Tallafi**

**01**

**Ba a yi ba**

**0%**

**Manyan Ayyuka**

# Muhimmiyar gudummawar lafiya ga tsarin inshorar lafiyar jama'a a mazaɓar dan majalisar dattijawa na Zamfara ta Tsakiya



N214m Ba a yi ba

Masu tantance ayyuka sun gudanar da cikakken bincike a faɗin mazaɓar domin tabbatar da aiwatar da wannan aiki. Amma, duk bayanan da aka tattara sun nuna akasin hakan. Daki-dakin rahotanni daga mutanen mazaɓar sun nuna ba'a aiwatar da aikin ba, wanda hakan a nan ke nuna wani gagarumin bambanci tsakanin aikin da aka tsara da kuma sakamakon aiwatar da shi a bayyane.

# MAZAƁAR ANKA/MAFARA

**Hon. Muhd Isa Anka**



**03**
Ayyukan da Aka Gabatar

**02**
An aiwatar

**75%**
Ayyukan Horo da Tallafi

**01**
Ba a yi ba

**25%**
Manyan Ayyuka

# Horas da matan karkara a kan amfani da makamashin zamani na sarrafawa da adanar abinci a mazabar tarayya ta Anka/ Mafara

Mazabar Anka/ Mafara

**N41m** **An aiwatar**

Dan majalisar, wanda ya samu nasarar lashe kujera ta ɗan majalisar tarayya a zaɓen shekarar 2023, ya aiwatar da wannan aikin ne a ranar 9 ga Maris, 2024, a otal din Karma dake Gusau. Sakamakon taɓarɓarewar tsaro a mazaɓar da kewaye, an kai mata guda hamsin (50) zuwa babban birnin jihar domin horas da su. Taron ya mayar da hankali kan ilimantar da mahalarta game da makamashin da ake iya sabuntawa da kuma amfani wajen sarrafa abinci da adanawa.

A karshen horon, kowace wanda ta ci gajiyar shirin ta samu murhu da kuma naira dubu ashirin (N20,000). Sai dai, ba a fayyace ƙa'idojin zaɓar mahalarta ba, kuma masu tantance ayyuka sun lura cewa da yawa daga cikin matan ba sa yin sana'o'in da za su ci gajiyar wannan tallafin. Wannan ya haifar da ayar tambaya game da tasiri aikin.

A ɓangaren kasafin kuɗin aikin kuwa, jimillar tallafin jarin da aka rabawa shine Naira miliyan daya. Duk da yake babu ƙayyadadden farashin kayayyakin da aka raba, gabaɗayan aiwatar da aikin bai dace da jimillar kasafin kuɗin da aka ware ma aikin ba. Don haka, wannan aikin ya gaza cimma gurin kwalliya ta biya kuɗin sabulu, kuma irin hakan yana haifar da shakku kan yin gaskiya wajen sarrafa kuɗin al'umma.














# Samar da na'urorin sana'o'i a mazaɓar Anka/Mafara

Mazabar Anka/ Mafara

N30m An Aiwatar

Aikin, wanda aka gudanar a ranar 9 ga Maris, 2024, a otal din Karma dake Gusau, ya haɗa da jigilar waɗanda suka ci gajiyar shirin su hamsin (50) daga mazaɓar da ke fama da rikici zuwa babban birnin jihar saboda dalilan tsaro. Taron horon ya mayar da hankali ne kan makamashi mai sabuntawa, musamman koyawa mahalarta yadda ake amfani da makamashin hasken rana don amfanin gida da kasuwanci, wanda kuma ya haɗa da horo a kan yadda ake harhaɗa na'urorin samar da makamashin. An yi niyyar ne cewa wannan tsarin horon zai ba mahalarta tushen ilimin yin kasuwanci.

Kowane mahalarci ya samu kyautar Naira dubu ashirn (N20,000) a karshen taron na yini domin su taimaka wajen fara ayyukansu. Duk da haka, masu tantance ayyuka sun kasa tantance ma'auni da aka yi amfani da shi wajen zaɓar masu cin gajiyar shirin, da kuma ko akwai wani tsarin sa ido na tantance ingancin shirin bayan an aiwatar.

Ta fuskar kudin aiki kuwa, jimillar tallafin jarin da aka baiwa waɗanda suka amfana shine Naira miliyan daya. Idan aka yi la'akari da yadda aka aiwatar da aikin gabaɗaya, wannan yana nuna rashin daidaituwa tsakanin kasafin kuɗin aikin da kimar ayyukan da aka aiwatar. Aiwatar da ainihin aikin bai yi daidai da kuɗin da aka ware ma aikin ba, wanda hakan ke nuna naƙasu ga tasirin aikin.














## Samarwa da sanya fitulun hanyoyi masu aiki da hasken rana a mazaɓar tarayya ta Anka/Mafara

Mazabar Anka/ Mafara

N50m

Ba a yi ba

Masu tantance ayyuka sun gudanar da cikakken bincike a faɗin mazaɓar domin tabbatar da aiwatar da wannan aiki. Amma, duk bayanan da aka tattara sun nuna akasin hakan. Daki-dakin rahotanni daga mutanen mazaɓar sun nuna ba'a aiwatar da aikin ba, wanda hakan a nan ke nuna wani gagarumin bambanci tsakanin aikin da aka tsara da kuma sakamakon aiwatar da shi a bayyane.

# MATAKAN BADA MATSAYI

Matakin A na duban ko an yi amfani da dabarun haɗin gwiwar jama'a kamar taron zauren gari don shigar da 'yan ƙasa a cikin tsarin

Matakin B na auna aiwatar da duk ayyukan da 'yan majalisa suka gabatar

Matakin C na duba yawan ayyuka tare da bambancewa tsakanin manyan ayukkan da kuma aiyukkan bada tallafi ko horo.

**Matakin A**
**40%**

**Matakin B**
**35%**

**Matakin C**
**25%**

Dabarun da aka yi amfani da su na ɗaukar maki daya (1) rashinsa kuwa sifili (0)

Ayyukan da Aka Aiwatar / Jimillar Yawan Ayyuka

Manyan Ayyukan da Aka Gabatar / Jimillar yawan aiyukka

# Sakamakon 'Yan Majalisa a Matakin A

Matakin A na duba ko hanyoyin hadin gwiwa da Jama'a kamar taron zauren gari don shigar da 'yan kasa a cikin tsarin tantancewa da aiwatarwa.

| Ɗan Majalisa | Matakin A |
| --- | --- |
| Sen. Ikira Aliyu Bilbis | 0 |
| Sen. Sahabi Ya'u | 0 |
| Sen. AbdulAziz Yari | 0 |
| Hon. Kabiru Amadu | 0 |
| Hon. Abdulamalik Zubairu | 0 |
| Hon. Aminu Sani Jaji | 0 |
| Hon. Muhammad Ahmad | 0 |
| Hon. Muhammad Isa | 0 |
| Hon. Sulaiman Abubakar Gummi | 0 |
| Hon. Bello Hassan Shinkafi | 0 |

# Sakamakon 'Yan Majaalisa a Matakin B

Wakilan da suka sami matsayi mafi girma a Matakin B sun tabbatar da cikakken aiwatarwa / aiwatar da aikin da suka gabatar.

| Ɗan Majalisa | Matakin B |
|---|---|
| Hon. Kabiru Amadu | 1 |
| Sen. AbdulAziz Yari | 1 |
| Hon. Aminu Sani Jaji | 1 |
| Hon. Bello Hassan | 1 |
| Hon. Sulaiman Gummi | 0.66 |
| Hon. Muhd Isa Anka | 0.66 |
| Hon. Muhammad Ahmad | 0.66 |
| Hon. AbdulMalik Zubairu | 0.50 |
| Sen. Ikira Aliyu | 0 |
| Sen. Sahabi Ya'u | 0 |

# Sakamakon 'Yan Majalisa a Index C

Wakilan da ke da matsayi mafi girma akan Matakin C sun ba da fifiko akan manyan aiyukka. Waɗanda ke da ƙananan matsayi sun bada fifiko ne akan ayyukan tallafi ko horo waɗanda ke da wuyar a tantance tasirin su.

| Ɗan Majilisa | Matakin C |
|---|---|
| Hon. Kabiru Amadu | 1 |
| Sen. AbdulAziz Yari | 1 |
| Hon. Muhammad Ahmad | 0.66 |
| Hon. Bello Hassan | 0.33 |
| Hon. Sulaiman Gummi | 0.33 |
| Hon. Muhd Isa Anka | 0.33 |
| Hon. Aminu Sani Jaji | 0 |
| Hon. AbdulMalik Zubairu | 0 |
| Sen. Ikira Aliyu | 0 |
| Sen. Sahabi Ya'u | 0 |

# Sakamakon Himmar 'Yan Majalisa Wajen Aiwatar da Ayyukan Mazaɓun Tarayya na Shekarar 2023

| Matsayi | Dan Majalisa | Mazaba | Sakamako |
|---|---|---|---|
| 1st | Sen. AbdulAziz Yari | Zamfara West Zone | 2 |
| 1st | Hon. Kabiru Amadu | Gusau/Tsafe | 2 |
| 3rd | Hon. Bello Hassan | Shinkafi/Zurmi | 1.33 |
| 4th | Hon. Muhammad Ahmad | Bakura/Maradun | 1.32 |
| 5th | Hon. Amin Sani Jaji | Kaura/Birnin Magaji | 1 |
| 6th | Hon. Sulaiman Abubakar | Gummi/Bukkuyum | 0.99 |
| 6th | Hon. Muhammad Isa Anka | Anka/Mafara | 0.99 |
| 8th | Hon. AbdulMalik Zubairu | Bungudu/Maru | 0.50 |
| 9th | Sen. Sahabi Ya'u | Zamfara North | 0 |
| 9th | Sen. Ikira Aliyu | Zamfara Central | 0 |

# ALƘALUMMA NA BIN DIDDIƘIN AYYUKAN MAZAƁU

| 15 | 0 | 0 | 8 |
|---|---|---|---|
| An Aiwatar | Ba a bi sawu ba | Ba a tantace wurin aiki ba | Ba a yi ba |

**23**

**JIMILLAN YAWAN AYYUKA**

# ALƘALUMMAN AYYUKA



## Yawan Kuɗin da Aka Kasafta

**N1.44bn**


**29**

Ayyukan Horo da Tallafi

**06**

Manyan Ayyuka

# Kason Ayyukan da Aka Kammala



ZamTracka

Data | Civic Advocacy | Social Accountability

Follow up and track implementation of public projects within your vicinity

Upload pictures, add comments, send feedback to institutions

Announce and share with your friends, family and thousand across the state

Continue to engage.

No. 40, Sadiqu Sadiq Road,
Tudun Wada, Gusau, Zamfara State.

f/t @ZamTracka

ZamTracka@gmail.com

# #AskQuestions